Prince William County PUBLIC SCHOOLS
Providing A World-Class Education

HAUSA

Zuwa ga Mahaifa/Mai Riƙo:

Muna farin cikin kasancewar ku membobin reshen al'ummar mu, inda ake magana da sama da harshina ɗari a yanzu. Makarantar Prince William County Public ta mai da hankali tuƙuru wajen bawa kowane ɗalibi *Darajar Tarbiyyar Ilimi ta-Duniya.* Tun da tarayyar dangi tana da mahimmanci ga waɗannan ayyukan, muna farin cikin bayar da wasu bayanan tushe don taimakawa dukkan iyaye da masu riƙo don samun fahimta da kasancewa dumu-dumu cikin tarbiyyar ilimin yaron su.

Ana bayar da dukkan abubuwan makaranta cikin Ingilishi; Ko ta wane hali, muna ci gaba da fassara mahimman daftarori da bayanai cikin sauran harsuna da aka fi buƙata a yankinmu.

Masu magana da yawancin harshina na iya fa'idanta daga mahimman bayanan da ake sabuntawa akai-akai a Rukunin Yanar Gizon Prince William County Public Schools—pwcs.edu—da kuma ɗaiɗaikun rukunan yanar gizo na makaranta. Duka suna da mashahuran kayan aikin Google Translation, suna aikin fassara cikin sama da harshina 50. Galibi fassarorin kwamfuta suna da illa, amma har ila yau suna ba da ingantattun hanyoyin hadi ga bayanan makaranta. Idan baku da kwamfuta a gida, kuna iya amfani da wata a kowacce laburaren jama'a.

Mafi mahimmanci shine, Reshen Hukumar Makarantar yana ba da dama ga ƙwararrun masu fassara don taimakawa mafi yawan masu magana na kowane harshe fahimatar daftarorin da suka ƙunshi mahimman bayanai dangane da haƙƙoƙin ɗalibi dana iyayen sa, nauyace-nauyace, abubuwan tsammani, da sauran lamuran da suka shafi karatu da fa'idodi da hidindimun da ɗalibai ke iya samu. Masu fassara na iya taimakawa da taron iyayen yara game da waɗannan lamuran don tabbatar da cewa an isar da bayanan kowa da kowa kuma an fahimce su. Ana ba da waɗannan hidindimun ba tare da biyan ko sisi na iyaye ba.

**Yi amfani da kowanne daga cikin waɗannan hanyoyin don samun taimakon da ake buƙata.**

- Akan layi—tafi translations.pwcs.edu
- Da kanku—ziyarci makarantar yaronku. Babu alamar rashin kasancewar mai magana da harshenku. Koyaya ma'aikaci zai yi amfani da fastar bayanai don taimaka muku.

DR. STEVEN L. WALTS
*Superintendent of Schools*

P.O. BOX 389, MANASSAS, VA 20108 • WWW.PWCS.EDU

A kowane matakai, za a nemi ku ƙaddamar da abubuwa masu zuwa:

- Sunanku da sunan yaronku;
- Makarantar yaronku, matakin daraja, da sunan mai koyar da shi;
- Mutumin da ( ta suna ko aiki) kuke son yin magana da shi, da kuma abinda kuke son tattaunawa; sannan
- Lambar waya da mafi kyawun lokacin da za a iya samunku.

Idan yaronku ya kawo saƙon neman ganawa daga makaranta; ko kuma kuna da burin tsara tattaunawa tare da malami ko kuma wani ma'aikacin makarantar, yi amfani da hanyoyin da ke sama don tambayar mai fassara don taimakawa da waɗannan mahimman maganganun. Wani zai yi muku raddi da zarar yuwuwar hakan ta samu.

Tarayyarku na iya haifar da managarcin canji a tarbiyyar ilimin yaronku, kuma muna alla-alla don taimakawa ta hanyar samar da wadatar waɗannan hidindimun a gare ku. Muna fatan wannan wasiƙar ta bayyana jajircewar Prince William County Public Schools ga yaronku dalla-dalla da kuma ku kanku. Ina da ƙwarin gwiwar cewa za kuyi tarayyar buƙatar mu ga kowane ɗalibi don samun Darajar Tarbiyyar Ilimi ta-Duniya.

Bisa tsarkin niyya,



Dr. Steven Walts
Shugaban Makarantu

*Yayin ziyartar pwcs.edu, duba surar duniya mai launuka daban-daban don isa ga shafukan da ke da mahimman bayanai da aka bayyana cikin wannan saƙon.

